💋💋💋💋💋💋
*HASSAN DA HUSSAINI*
💋💋💋💋💋💋

By

Haj Maryam

Page 1

Wasu kyawawan samari na hango a wani katafaren gida dan da ka gani kasan gidan sarauta ne .

Wata mata ce kyakyawa ajin farko yar gajera fara sol da ita humm Maryam kenan macce mai ji da izza da son iko.

Maryam ji take tafi kowa a duniya saboda kawai tana auren dan sarkin Kaduna wato Hassan.

Yauma kamar kullum Hussaini nahango abakin wata bushirya mangwaro yana kuka yana gayawa abukanan sa tunda Hassan yayi aure ya juya mashi baya.

Daya daga cikin aboken mai suna Yusuf yace "haba Hussaini kaima kayi aure kadena sawa dan uwanka".

Budar bakin Hussaini sai  cewa yayi " abokina baka gane bane dama ni tun farko nbason Maryam dan batayi mani ba"ya karashe fada tare da jan tsuki mtwsss.

 Dariya Yusuf yayi"to wa kakeso ya aura?"ya tambaye shi yana dan duban shi cike da mamaki.

"Ga Chamsiya nan ko ita ba macce ce ba ai tafi Maryam komi"ya fada cikin dan gaga murya.

" A ganinka ba shi dai Maryam din ya ke so"Yusuf ya fada tare da tashi ya nufi inda ya aje motar shi.

Maryam ce zaune ita da masoyin ta Hassan  suna hira cike da so da kauna da kuma shaukin juna.

Hussaini ya shigo falon direct inda suke ya nufo,Hassan ya kura mashi ido yana kallon shi ganin duk ya rame hasken fatar shi ya kara fitowa sai yayi wani fayau.

 "Good morning!ya fada tare da zaunawa a kujera mai facing din su,amsawa sukayi cike da kulawa,Maryam kuma  ta tashi ta shiga kitchen.

Abinci ta shiga jerawa a dan karamin table ta turo gaban  Hussaini ture table din yayi abinci ya zube ji kake rugugugu duk kwanonin sun zube a kasa.

A hasale Hassan ya mike ya nufo......

Your comment please in yayi maku zan cigaba😁😁😁

Taku ce Haj Maryam💃💃💃💃💃
💋💋💋💋💋💋
*HASSAN DA HUSSAINI*
💋💋💋💋💋💋

By

Haj Maryam

Bismillahirahmanirahim

Page 2

A hassale Hassan ya miqe har ya daga
hannu kuma ya sauke, "Hussaini ka ga dai kai dan uwana ne, inason ka ina k'aunar ka amman soyayyar da ni ke maka ba zata bari in tsaya ina gani  kana wulaqantamin matata ba,ka sani Maryam matata ce  amanar ta aka bani kuma inason ta bantaba sanin dadin soyayya ba sai akanta kuma wlh zan iya sa6awa da kowa akanta saboda haka inason  daga yau karunqa girmamata ka dauketa amatsayin anty ka mudin kana so mu zauna lafiya".

Tinda ya fara zuba Hussaini ya daskare wuri guda yana kallon Hassan cike da mamaki.

 "Har bada Maryam ba anty na ba ce kuma batada darajar da zan girmamata" Hussaini ya fada tare da nufar hanyar fita.

Yana isa gida ya samu momy a main falo tana kallon TV.

"Hussaini zo nan" momy ta fada tare da nuna mashi wuri kusa da ita.

zuwa yayi ya zauna y'a sunne kai,murya ta na tsinkayo tana cewa" wai kai Hussaini yaushe zaka girma? kullum kana girma kana cin qasa"dagowa yayi yana kallon ta kafin ya ce "momy mi nayi Kuma?".

 " Rufe min baki ai kafi kowa sanin abinda kayi,to abinda zan gaya maka ka fita da matar aure tunkafin ranka ya bace,in kuma kaqi zan hada ka da yar qawata zainab atiku yarinya mai ankali

ga nutsuwa,"

"Gaskiya ni momy babu mai mani auren doli".

" Shine kuma kake matsa ma dan uwanka ya auri wadda bai so,to wlh bari Alhaji ya dawo mu tsara yadda za ayi in ya so  ka korota in an kai maka ita tashi kabani wuri".

Fuuu ya tashi yana gunguni direct part din shi ya wuce nan  ya hau kuka"ni mi zanyi da zainab wallah babu mai mani auren doli".

Asalin labarin....

Maryam Salis shine cikaken sunanta, asalin su yan zanfara ne suna zaune a unguwar gada biyu.

Mahaifan Maryam talakawa ne,sai dai ita Maryam Bata aje kanta kusa ba yar karya ce ba ta aje komi ba sai girman kai ga son a ce ita wata ce.

Cikin qarya da Maryam ta sa ma kanta har da k'in makaranta gwamnati ita ala doli sai privé ta ya'ayan masu kudi,ganin mahaifan ta basuda hali ta tatara karatun ta watsar.

Yanzu babu abinda take sai abkin tara samari kuma akasarin su duk t yayan masu kudi ne amman abinda bata sani ba duk cikin babu mai  sonta da aure........

Taku ce Haj Maryam Aliyu Yahya
💋💋💋💋💋💋
*HASSAN DA HUSSAINI*
💋💋💋💋💋💋

By

Haj Maryam

Page 3

Bismillahirahmanirahim

Suwa ye Hassan da Hussaini????

asalinsu suyan kaduna ne,mahaifinsu Alhaji Muhammadu cikakkun yan sarauta ne masarautar

su ta dauko asali ne tun daga kakan su alhaji Ayuba dattijon arziki gason talakawa azamanin mulkin shi.

Talakawa suna son shi saboda yanada tausayi,ga babu kyarmar na kasa dashi.

Ya auri mata shi mai suwaiba inda zaman auren ya kasance cike da soyayya da kaunar juna, sai da suka kwashe sama da sheka goma Allah bai basu haihuwaba.

Tin hankalin su bai tashi har dai suka bazama neman magani inda har takai da sunyi neman magani har sun gaji suka zuba ma saurauta allah ido.

Rahama ubangiji bata yankewa,rana daya Suwaiba ta tashi da zazzabi hankalin Alhaji Ayuba ya tashi sosai.

Suna zuwa asibiti a gwajin farko aka gano Suwaiba nadauke da ciki na tsawon wata biyu

Zo kuga murna wajan alhaji Ayuba,dan tsabar murna sai da ya bidi zaucewa dan yaji dadi sosai wanda bai milsaltuwa.

Ko da suka dawo gida sukaci gaba da renon cikin su,akwana atashi harcikin Suwaiba yashiga watan haihuwar.

Wata ranar litinin suwaiba ta tashi danaquda,tin tana daurewa har ta kasa ta gayama mijinta.

Zuwansu asibity babu wuya s ta haifi danta mai kyau mai kama da mahaifin shi.

Ranar suna akasawa yaro suna Muhammadu.

Tin lokacin da aka haife shi bai sans wani abu rishi ba,ya taso cikin gata da so da kauna wanda iyayen shi nuna mashi.

A kwana a tashi babu wuya wurin allah Mahammadu yayi karatu secondary na school nan Alhaji yatura Shi qasar waje dan cigaba da karatun shi.

A can America ma Muhammadu ya maida hankalin shi akan karatunshi inda ya karanci aikin likitanci.

Tin kan ya dawo mahaifin shi ya gina mashi katuwar asibiti a nan gida Nigeria yabude mai suna Muhammadu clinic Hospital agarin kaduna.

Yau kama kamar kullum yadowo daga aiki ya iske mahaifinshi falow zaune Yana huta ya duqa har kasa yace" baba sannu da hutawa"dagowa mahaifin nashi yayi yace "yauwa son" ya fada yana dan murmushi.

Gyaran murya alhaji Ayuba yayi "alhamdulillah godiya ta tabbata ga Allah daya nuna mani wanan rana da  ka gama karatun ka lafiya yanzu abinda yarage shine kafitar da matar aure".

Dan sadda kai kasa yayi kafin yace " to baba insha Allah"........

Haj Maryam takuce
💋💋💋💋💋💋
*HASSANA DA HUSSAINI*
💋💋💋💋💋💋

By

Haj Maryam

Page 4

Wannan fage din nakane Hussaini 80k bawan mata🤪🤪

Bismillahirahmanirahim

Muhammad yace "to
To baba insh allah zanyi qoqari infitar da matar aure ciki yan kwanakin nan"," allah yayi maka albarka"shine abinda mahaifin shi yace.

Muhammad ne ke shiri a gagauce domin zuwa asibiti.

Tuki yake ahankali can ya hangi wata kyakyawa tana tafiya cikin nutsuwa, tunda yagan ta yaji ta shiga ran shi.

Dan matsawa yayi kadan yayi parking motar shi daf da ita ya sauke gilas yace"Assalamu alaikum",dan tsayawa tayi tace" wa alaikassalamu".

"Dan allah in ba zaki damu ba ina son sanin sunan ki" dan kallon shi tayi alamun shi ya fara gaya mata nashi mana,
" ni sunana Muhammad to ke fa?" tace nikuma "hauwa'u" ,"nice name!amman ina zuwa haka?".

"Makaranta zani".

" ok ki shigo in rage maki hanya mana".

"A'a na gode babu matsala zan samu adaidaita".

"haba malam hauwa ki daure ki shigo mana"

Nan dai ta shiga,"malama hauwa'u zan iyasanin gidanku?"

"Eh Mana, a malali gidan mu ya ke ",a nan ya anshi number ta ya wuce asibity.

Bayan haduwarsu dakwana biyu ya shirya zuwa unguwar malali ya nazuwa ya kira number da ta bashi tana dagawa tayi mashi kwatance.

Yana Isa qofar gidan su ya iske mahaifinta zaune a kan tabarma yana shan iska,zuwa yayi ya duqa har qasa ya gaishe shi.

Bayan sun gaisa cikin mutunci Mahaifinta yace "sai dai ban gane ka ba yaro" yace "eh nazo gun hauwa'u ne" ya fada yana susar keya.

Yace "Masha Allah daga ina ?"

"ni dan gidan sarki Alhaji Ayuba ne kuma da niya auren ta nazo".

Mahaifinta yace " ba matsala in dai tana son ka"ya fada tare ta tashi shiga gida ya turo mashi hauwa'u.

Tana fita ta tarar dashi suka gaisa tare da yin hirara ta masoya.

Yana isa gida bai wuce ko ina ba sai wajen mahaifin sa anan yakwashe duk yadda suka da baban hauwa'u ya gaya mashi.

Mahaifinsa yaji Dadi sosai yace" insha Allah gobe za aje gidansu ayi magana"

Washe gari takama ranar laraba qanin mahaifin shi suka je gidan su hauwa'u kasancewar baqananan mutane ba anan aka tsai da maganar aure wata biyu.

Akwana atashi wata 2 kamar yauce agurin Allah yau juma a aka daura auren Muhammadu da hauwa'u.

Anyi biki nagani nafada anci an sha a ngama lafiya a ka kai amarya dakinta.

Bayan aure dashe Kara biyu  hauwa'u ta haifi yaran ta yanbiyu Hassan da Hussaini kyawawa farare tasss .

Haka su ka tashi cikin so da kaunar junansu sai dai ko wane da nashi hali, Hassan yatashi da haquri Hussaini yatashi da fada ga kishin dan uwanshi.

Komi tare ake masu ba a banban tasu Amma kullum Hussaini gani yake anfison Hassan sun tashi cikin gata dakulawa bawajen kakanniba Baga iyaye ba dayan uwakowa sonsu ya keyi.

Sai da suka kwashe wajan shekara goma a duniya  sanan hawa'u ta kara samun wani ciki......

Ta kuce Haj Maryam 😄
💋💋💋💋💋💋
*HASSAN DA HUSSAINI*
💋💋💋💋💋💋

By haj Maryam

Wannan page din na kine Nafissa Laouali Rabo

Page 5 to 10

Bismillahirahmanirahim

Sai da suka kwashe shekara goma a duniya sannan mahaifiyar su ta qara samun ciki.

Samun wannan cikin ba karamin farin ciki  familyn su kayi ba,dan murnar su bai musaltuwa.

A kwana a tashi yau cikin momyn su ya cika wata takwas nan mahaifin su ya kwashe su zuwa India a can mahaifiyar su ta haifi yarinyar ta mai kyau, ranar suna yarinya taci sunan Nana a nace mata Hamdala.

Su kuma Hassan da Hussaini suka cigaba da karatunsu a can.

Tunda a ka haifi Nana dukannin su suna nuna mata soyayya dan ba karamin so suke mata ba.

Bayan shekara goma sha biyar kakan  su ya kamu da rashin lafiya,shi yayi sanadiyar dawowar su Nigeria.

Inda yanzu su twins suna da shekara 25,Nana Kuma tanada shekara 15 .

Bayan dawowar su da sati biyu Allah yayi wa kakan su Alhaji Ayuba rasuwa.

Jama'a da dama sunyi kukan mutuwar me martaba musamman ma talakawa,familyn shi kuma ba a magana.

A kwana a tashi yau
Alhaji Ayuba ya cika shekara daya darasuwa inda a ka nada mahaifin su a ka bashi sarautar kakan su.

Yau ta kama ranar asabar Hassan da Hussani sun shirya zasu gida abokin su Nafi'u.

Suna kan hanyar suta tafiya Hassan  yayi saurin taka birki "kuuuut!"wanda yasa Hussaini ya firgita tare da cewa"ya dai lafiya zaka tsaida mu kan titi?".

Hassan kasa cewa komi sai nuni da yayi mashi da dan yatsan shi ,hurin da ya nuna yabi da kallo wata kyakyawar matashiya na hango gajeruwa fara sol da ita sai sheqi take.

Marfin motar ya bude ya qarasa  wurinta tare da yi mata sallama,cikin yanga da jan aji ta amsa mashi tare da yin shiru hakan ya bashi damar cigaba da cewa "my name is Hassan,you fah?".

cikin yauqi tace"ni kuma Maryam", dan murmusawa yayi yace" nice name ,daga wacce unguwa kike ?"

"Ni ba yar nan garin ba ce
bikin qawata ne ya kawo ni", " ah ok ina kuke bikin?inji Hassan,kai tsaye ta bashi amsa da "unguwar dosa GRA ".

"Masha Allah
zan iya samun number ki?" ta daga mashi kai alamun eh nan ta karanto mashi.

Duk abinda suke Hussaini na tsinkayan su ta glass din mota tunda ya ganta yaji yatsaneta shi haka kawai bata burge shi ba...

Tunda Hassan ya koma gida bai da magana sai ta Maryam ko hira ya ke sai yasa Maryam daga ya fara Hussaini ke barin wajen kwatakwata baya qaunarta .

Yau ta kama Monday an gama biki Maryam ta koma gida,kullum Hassan sai ya kira wayar ta,yauma da sukayi waya ya mata alqawari zai je gidan su.

Haka ko akayi ranar juma'a ya shirya ya tafi gusau inda ya samu tarbar arziki,sun sha hirar soyayya da qauna a nan ya tabbatar mata da aure ya ke sonta bai sha wuya ba wajen amincewar ta ba saboda burin Maryam har kullum bai wuce ta auri me kudi ba balle ta samu dan sarki kullum sai girman kai daji da kai....

Taku ce haj Maryam
💋💋💋💋💋💋
*HASSAN DA HUSSAINI*
💋💋💋💋💋💋

By haj Maryam

Wannan page din na ki ne Chamsiya Laouali Rabo🤪🤪🤪

Bismillahirahmanirahim

Page 12 to 15

Bayan maganar su da kwana biyu dadyn su ya kira Hussaini "ina umartar ka da kayi gagawar fitar da matar aure dan a hada ka da dan uwanka" cewar dady ya fada tare da tamke fuska alamun babu wasa.

Budar bakin Hussaini sai cewa yayi" gaskiya ni dady ban shirya aure yanzu ba".

Dady yace "rufemin baki sakarai,wlh indai zakaci gaba dawanan halin kanada tashi ka bani waje".

Yauma kamar kullum mahaifiyar zainab ce na hango zaune kusa da momy su Hassan ,tana cewa "ya  maganar auren Hussaini da zainab dan magana ce ta kkawo ni,
zainab nanan ko abincin kirki bataci saboda Hussaini kullum kuka takeyi Dan Allah hajiya mai zai hana ayi auren su da wuri  a huta?"

"Hmmm"cewar hajiya " wlh qawata yaron ne ka haifeshi baka haifi halin shin ba,na rasa ya zanyi da yaron nan kullum taurin kanshi qaruwa yake,amma dan Allah ki bani lokaci zamu san yanda zamuyi"

"Toh" kawai  maman Zainab tace.

Yau a kaje a ka nema ma  Hassan auren Maryam kuma sun samu,daman mahaifin Maryam abinda ya ke so kenan ya kawar da ita kafin ta jawo mashi abun kunya.

Hassan da Maryam ko wata shaquwa da qauna ke qaruwa a zuciyoyin su kullum Hassan natarairayar Maryam duk da halinta nakwadayi daroqo amma Hassan  bai ganin aibun ta.

A kwana  a tashi har an fara shirye_shiyen auren Maryam da Hassan komi shi yayi mata,yayi mata lefe nagani nafada harta da kayan daki yace zai yi mmata komi,wannan ya kara hura hutar qiyayar ta a zuciya Hussaini dan shi   ya tsani macce mara kamun kai wadda batada aikin yi sai roqon samari.

Maryam ko ta je ta samu mahaifiyar ta da zancen Hassan yayi mata Alqawarin zai mata komi.

Mahaifiyar ta tace "ban yarda ba,ba zan saida maki da darajar ki ba a gun dangin mijin ki ba,duk da muna talakawa zamuyi komi na mu daidai gwargwado".

Budar bakin Maryam sai cewa tayi " gaskiya ni bana so saboda ko za a yi mani baza amin wanda yakai shiba,gaskiya ai ina zuwa gida qawayena ina ganin nasu so kike yi suzo su mani dariya ga Hajara Aj anyi mata kaya mai tsada ga Aisha maman nawal nan itama haka sai ni gaskiya ni abari yayi mani"Maryam ta fada tana turo baki gaba.

Babu yadda mamata batayi ba dan ta fahimtar da Maryam illar hakan amman taqi.

An fara shiye_shiyen biki ammar ya ta sha gyara inda ango ya bude mata bakin aljihu.

Yau ta kama ranar kamu qawayen amarya duk sun hadu amarya tasha kyau domin ango ya kawo mata mai kwalliya Lina gwanar iya kwalliya ce.

Anci an sha galgale ansha inda qawayen amarya suka zage dan tsewa Jen rawa

Abun dai baki bai iya misalta shi har ta da yan uwan Hassan sun zo sun ga amarya ta zage damtse tana kwasar shoki abun bai wani ba su haushiba tinda su yan boko ne in ka fida Hussaini da ya dauki hakan rashin kunya.

Anyi taro lafiya an watse lafiya.

Yau ta kama ranar lahadi,ranan kuma a ka daura auren Hassan da Maryam akan sadaki dubu dari

Maryam amarya na gani tana shirin zuwa reception bayan miti ishirin sai ga motar ango ya zo daukar Maryam.

Wucewar su keda wuya Hussaini na hango da abukanan shi yana cewa "wallahi baza ayi taron an lafiya ba tunda tace kwadayi ne aikin ta,to ni ku sai na lalata masu wannan taron".

Muryar Yusuf na tsinkayo yana "haba Hussaini kai da yaci ace ka taya dan uwanka farinciki amman kai ne zaka batamai taro?"

Budar bakin Hussaini cewa yayi "malam ba wa'azi nace kamin ba idan ba zaka taya ni ba ka bar ni".

Isata hol din taro yayi taro qawayen ango suntaru inda na hango Muhammadu Shafi'u babban abokin ango tare da Nazifi yarima, a gefe guda kuma Yan group din MSHELIYAS  sunyi gungun su daban Aisha humaira sai surutu take kamar akun kuturu😜.

Fannin amarya ko qawayen ta kowa yayi shiga ta alfarma,su Aisha maman nawal su hajara Aj ina daga kaina na hango Asmau ban yi mamaki ba dan naga yan group din MATA MASU AJI,gefe daya kuma MATAN GIRMA nagani su Aisha Ibrahim su ummu Hasina.

Muryar mc naji" za mu bude taron mu da suna Allah Yanzun  muna so muga amarya da ango".

Isowar amarya da ango a kan filin ke da wuya wutar hal din ta dauke gabadaya .

Dede lokacin da aka kunna wutar wajen Hussaini nagani yakwace sifika ahannun m c budar bakin Hussaini yace.....

Yanzu gam zai fara🤪🤪🤪

Kubiyoni a page nagaba muga mai Hussaini zai yi, zai cika burin shi ne na ganin ya wulaqanta Maryam ko kuwa🤪🤪

Haj Maryam takuce
💋💋💋💋💋💋
*HASSAN DA HUSSAINI*
💋💋💋💋💋💋

By haj Maryam

Page 15 to 20

Bismillahirahmanirahim

Karbe sifikar Hussaini yayi yace "ni sunana Hussaini wanda ku ka fi sani da 80k,

Nariga nayi Alqawarin Hassan ba zai ta6a auren Maryam ba ,

Amman tunda ta dake seda ta aure shi to wlh tallahi ba zata samu zaman lafiyaba,

Kuma nayi Alqawarin...."wuf naji an amshi sifika a hannun shi ko da nakai kallona gefen wata tsaleliyar yarinya matashi mai kyau.

Tace "ni sunana chamsiya nice wacce keson Hassan kuma nayi Alqawarin Sai na aure shi ko ta wane hali" ta fada tare da miqawa takusa da ita .

"Ni kuma sunana Aisha humaira nice babbar qawar Chamsiya kuma munyi alqawarin bata goyon baya dari bisa dari",nan sauran qawayenta suka amsa duk suka gabatar da kansu sunna gamawa Hussaini yace" ina umartar kowa yabar wajen nan".,

Nan wata babbar qawar amarya ta miqe" babu mezuwa ko Ina kuma ku kunyi kadan  ku lalata mana biki"ba ta ida rufe baki ba naji  tass Hussaini ya watsa mata mari daga hannu tayi  zata rama chamsiya tariqe ta "ke wawuya karki saki ki mari qanin mijina"

Budar bakin Aisha maman nawal tace" shi bai ji kunyar marina ina matar aure ba sai ni zanji kunyar ramawa?".

Nan dambe yabarke tsakanin qawayen chamsiya da Maryam anyi kacakaca da hol duk an kori jama'a , chamsiya ta dauki cake tawatsawa Hassan afuska ganin haka amarya taa tashi ta nufeta.

"Wallahi zan dau komi
amma bazan yarda awula qanta Hassan ba "

Nadanbe yakachame tsakanin amarya Maryam da chamsiya .

Mai martaba na zaune a fada wani bafade ya fado da dugudu Allah yaba ka yawan Rai balafiya Nan yagaya mashi duk Abunda ke faru.

Anan mai martaba yayi umarni da fadawa suje wajjen .

Koda fadawa suka iso anyiwa amarya kacakaca shi ko Hassan tunda ya daskare guri daya komotsi bai yi ba sai shigowar fadawan ne ya dawo daga dogon suman zaunen da yayi.

Nan fadawa suka kori kowa a kamaida amarya gida.

Tunda amarya ta isa gida take kuka tana danasanin auren Hassan bata taba sanin qiyayyar dangin miji haka take ba sai yau .

Jama'a suka shirya aka kai amarya,abokan ango na watsewa sai ga su Hussaini suna shigowa Hussaini yafara watsawa Maryam mari "wlh tunda kika aure dan uwana wallahi kinta rarwakan ki
wahala "

Bai gama rufe baki ba sai chamsiya da qawayen ta suna shigowa Hussaini yace duk kayan da ke gidan Nan kufarfasa shi ai ba daga gidan ubanta tazo da suba.

Nandanan komi ya hargitse suka fara buge_buge .

Show glass da kayan kallo duk seda suka fasa seda suka tabbatar sun fasa komi sunba amarya kashi.

Har ango da yazo dakartar dashi dede lokacin Aisha humaira tacillon plet se agoshin Hassan

Nan jini yabarke
Ko da suka bar gidan daqyar Hassan ya iya daga waya yakira momy su
.
Momy nazaune kiran Hassan yashigo Yana mata bayani najitace "innalillahi wa Inna ilaihi Raji un "

Kode Hussaini so ya ke ya kashe ni ne nan takwashi fadawa sunna Isa suka iske Maryam asume ,aka kwashe su se asibity suna shiga nurses suka dauketa zuwa Emargency tun da suka shiga ake ba maryam taimako amma har yanzun bata farfado ba........

Haj Maryam takuce
💋💋💋💋💋💋
HASSAN DA HUSSAINI
💋💋💋💋💋💋

Duka littafin Nan nasadaukar dashine gareka uban gidana Hassan ATK

By haj maryam

Fage 20 to 25
End

Wannan fage dinnakine Anty Aisha my sweet sister

Bismillahirahmanirahim

Tunda aka Kai Maryam asibity Bata farfadoba haryan zun

Tunkoma war momy su gida

Tayi ma mahaifinsu magana akan tanaso adaura auren Hussaini da zainab

Mai martaba yace insha Allah ranar juma  a za a daura

Auren shi da zainab zamu gani inshi yahaifemu

Satin maryam daya cif a asibity sannan ta farfado washe gari aka sallame su suka koma gida

Sede me martaba yasa angyara mata gida Kuma yasiya mata sabbinkaya Nan Hassan da Maryam aka bude sabon rayuwa mecikike da soyayya da qauna

Sukaci amarcin su hankali kwance yauta takama ranar alhamis

Dady su yazaunar da Hussaini yayi maina siha  inde harni na haifeka banyarda kaqara shiga Sha a nin rayuwar auren Dan uwankaba

Kuma gobe insha Allah za a daura auren ka da zainab cewar dady su

To Hussaini yace Yana turo baki gaba

Washe ga Ana idar da sallar juma a aka  daura auren Hussaini da zainab

Gidan su zainab sunyi taro sunyi biki sosai sabanin gidan ango

Inda Hussaini bema San anayiba kwata kwata bema shigo gidan ba tunda suka fara Sha ani

Anyi taro anwatse ankai amarya dakin mijinta

Saide tunda aka Kai amarya ango be wai wayetaba kullum se dai yaje gidan abokan shi yakwana

Akwana atashi yau watan zainab uku Amma ango betaba zu gidan amarya ba

Yauda wowar Nana daga gidan take gayawa momy komi

Nan momy takishi

Wallah Hussaini zansaba ma cewar momy Kuma wallahi daga yau inaso karunqa zuwa gurin matarka

To najiyo Hussaini yace canqasan maqoshi

Yanatashi be zarce ko inaba se part dinshi

Yana shiga wani dadda Dan kamshine yadaki hancinshi

Kallo gefen shida yayi zainab yahanga

zaune tana cin abinci wani hadiyar miyo yayi sakamakon ganinta da yayi cikin lafiyayyun kayan bacci masu daukar Hankali

Dagokai zainab tayi sukayi ido biyu da Hussaini

Cikin rawar murya tace sannu da zuwa

Yauwa ya amsa mata atakaice yawuce bed room dinshi tunda yadaura idon shi akan zainab yauce

Rana tafarko daya farajin wani Abu akanta

tunda yashiga daki yakasa rintsawa Yana rufe ido surarta yakegani

Semamaki yakeyi Ashe haka take

Kullum baya iya barci yau satin su biyu kenan suna zaune ahaka

Hussaini na hango Kwance yanata juyi Amma barci yaga gara kawai

Yauze yasame ta ayita ta qare zainab nakwance adakinta tana chat jitayi anbude qofa Adan razane tamiqe ganin

Hussaini tayi tsaye akanta budar bakinta malam yafiya

Lafiyarce takawo haka cewar Hussaini nazo inkabi haqina

A danrazane zainab tamiqe bangane mekake nufiba

Zaki gane cewar Hussaini danmatsawa yayi kusa da ita ka Dan

Ban ankaraba naji zainab tadiro akan gado

Duk iya qoqarin da Hussaini zeyi Dan yashawo kan zainab

Yayi Amman taqi

Yagaji daroqo dama giya yakoma yimata wa azi

Nadai daqyar yashawo kan zainab

Nikuma inagani sun sulhunta nagashe musu wuta naja musu qofa na urufe

Washe gari da sassafe nahango Hussaini nagyaran gida yayi wanke wanke da shara hargoge goge fuskar nantashi cike da annuri

Faran ciki yabayyana afuskarshi Yana gama hada mata break fast

Yazauna yayi ta gumi Yana tunani asha haka aure keda Dadi Aida nasan haka yake

Datuni nabari an hada Dana Hassan

Gaskiya nayi  kuskure da nake shiga tsakanin masoya

Akwana atashi bawuya agurin Allah yau sheka biyarkenan da auren
Hassan da
maryam

Nan hango wasu yara yandu Gul dugul guda uku

Macen ce tasheqo da gudu Abba Abba kaga kanzillahi ko

Budar baki abban nasu yace zo Nan Afra kaima kanzillahi zona bana Hana kufa ba affan yace Abba wallahi afrace bataji

Abban Yan uku wallahi bakwa gajiya da shirme ce war maryam

Hassan Naga yataso Ina zan gaji tunda yauma inaso aqara samomin Yan uku Nan yariungumeta yanawa Allah godiya

Umma umma cewar
Yasmin zainab na hango akici tanace wa karku shigo minnan kuwuce gunbaban ku Hussaini na hango Yana cewa kuzo yayan baba

Haba abban Minal wallah nina gaji kullum abudaya komi Kai Minal wallah banso kasha gwabata

Cewar chamsiya

Budarbakin abban Minal yace bari insha gwaba abuta

Tunda Hussaini yayi aure chamsiya matayi aure Da nafiu Nana ko ta auri Dan abokin abbansu

Kuma suna zaune lafiya

Alhamdulillah anan nakawo qarshe labarina inagodiya ga Allah dayabani

Ikon kammala wannan labari

Ina godiya ga Anty chamsiya

Masuce wa inkwatanta a dallaci tsakanin Hassan da husaini Dan nafison Hassan

Wlh da Hassan da husaini duk daya suke awaje bawanda yafi wani

Kuma duk inason su irin so  na addinin musulunci

Wannan littafin nasadaukar dashine

Gabadaya gareka uban gidana Hassan ATK Allah yajamana kwananka

Se mun hadu Alittafi nagaba

Haj Maryam takuce